# Ra’ayoyi Daban-daban

Mahalarta taron za su duba rawar da ra’ayoyin mutane ke takawa a lokacin kimanta bayanin da aka haɗa da kasuwancinsu na intanet ko kuma kasuwancin wasu mutanen a intanet. Za a wayar masu da kai dangane da dalilan da suka dace (misali., lokaci, al’adu, zamantakewa, na cikin gida / yanki / duniya) da ya yi tasiri a kan kasuwancin intanet ɗin wani. Bugu da ƙari, mahalarta taron za su yi la’akari da matsalar da bayanin da suka sanya a intanet zai jawowa dangantakarsu da iyali, abokai, da masu wakiltar hukuma (misali., malamai, ma’aikata).

## Ma'aikata

Gano Yanda Fuskar Rubin Take
Takardar Darasi a Kan Furofayil Ɗin Dandalin Sadarwar Zamanin Kassra

# Mene ne Ra’ayi?

## Kashi Na Ɗaya

### Hoton Tattaunawa a Aji

Gabatar da wasu hotuna mabanbanta a kan yanda fuskar Rubin take a kan a allon majigi. A lokacin da kake yin tambayoyi, nemi mahalarta taron su fito sannan su nuna wane hoto ne suka gani

### Tambayi Ɗalibanka

Me kake gani a lokacin da ka kalli wannan hoton?

Ku nawa ne kuka ga gilashin?

Ku nawa ne kuka ga fuskokin guda biyu?

Shin za ku iya ganin duka biyun a lokaci guda?

Abun da za ka gani ya danganta ne da ra’ayinka. Me kuke ganin ra’ayi ke nufi?

### Tattaunawa a Aji

Rubuta ma’anonin da mahalarta taro suka bayar a kan allo.

### Sanar da Ɗalibanka

Ra’ayi wata irin ɗabi’a ce a kan wani abu; ra’ayi.

## Kashi Na Biyu

### Sanar da Ɗalibanka

Ga wani misalin. Kamar a ce abokinmu Azul ya samu nasarar shiga ƙungiyar wasan ƙwallon ƙafa a makaranta. Lokacin da ya sanar da mahaifiyarsa, ya ce, “na samu nasarar shiga ƙungiyar wasan ƙwallon ƙafa!” mahaifiyarshi ta yi alfahari da shi ƙwarai.

Lokacin da Azul ya sanar da abokinsa, Raviv, cewa ya yu nasarar shiga ƙungiyar, Raviv ya ce ya yi wa Azul murna sosai.

Haka kuma Azul ya sanar da abokinsa Val cewa ya yi nasarar shiga ƙungiyar wasan ƙwallon ƙafa. Val, duk da haka, ta yi ƙoƙari, kuma Azul ya gano ta a lokacin. Saboda haka, Val ba ya farin ciki.

Haka kuma Azul wani mamba ne a cikin kulob ɗin kimiyya, kuma zai rasa wasu tarurrukan da za a yi kulob ɗin kimiyya domin ya samu damar halartar wurin koyon ƙwallon. Lokacin da ya sanar da Dani, shugabar kulob ɗin kimiyyar, ita ma ba ta farin ciki sosai.

Duk waɗannan mutanen a rayuwar Azul sun ji labari iri ɗaya: Azul ya samu nasarar shiga ƙungiyar wasan ƙwallon ƙafa.

**Tambayi Ɗalibanka**

Me yasa suka bambanta wajen ra'ayinsu?

Me yasa bambancin ra'ayoyinsu, da nau'o'in dangantakarsu ga Azul, ke da muhimmanci?

Shin za ka iya tuna wasu misalan na yanda mutane daban-daban za su iya yin tunani daban-daban a kan abu guda?

Me yasa ra'ayi ke da muhimmanci?

# Yanayin Yin Tunani

## Kashi Na Ɗaya

### Tattaunawa a Aji

Rarraba mahalarta taron zuwa ƙungiyoyi na mutum 3-4. Ba kowace ƙungiya takarda da alƙalama ko fensura.

### Sanar da Ɗalibanka

Zan ba kowace ƙungiya takardar darasi tare da furofayil ɗin dandalin sadarwar Kassra da aka ƙirƙira da kuma wani fallen takarda. A kan fallen takardar akwai sunan wani wanda ke cikin rayuwar Kassra. Ma matsayin ƙungiya, ka yi tunani cewa kana kallon wannan furofayil ɗin dandalin sadarwar zamanin ta cikin idanun mutumin da ke kan fallen takardar. Me kake tunani a kan Kassra? Me za ka iya cewa a kansa? Me yake so? Mene ne ba ya so? Me ya yi jawabi a kai? Mene ne ra'ayinka a kan Kassra, dangane da ra'ayinka? Kana da mintuna 10. Ka shirya domin gabatarwa a ƙarshe!

Nemi kowace ƙungiya ta gabatar.

Rawar da mutane ke takawa/mutanen da ke rayuwar Kassra:

1. Mahaifiyar Kassra, wa ya damu da lafiyar ɗanta.
2. Aminin Kassra, wanda ke duba shi.
3. Wata yarinya a makarantar da ke maƙwabtaka da shi, wadda ba ta san Kassra ba.
4. Malamin Kassra.
5. Wani shugaba wanda zai ba Kassra aiki.

### Tambayi Ɗalibanka

Wasu hanyoyi ne suka bambanta yanda ka ɗauki Kassra da kuma yanda ka kimanta Kassra?

Me yasa kake ganin akwai waɗannan bambance-bambancen?

Shin kana ganin dukkan waɗannan abubuwan da aka kimanta daidai ne? Me yasa/me zai hana?

Shin za ka iya tuna lokacin da wannan ya faru a rayuwarka — lokacin da aka bayyana bayani ɗaya ta hanyoyi daban-daban ga mutane daban-daban?

**Tambayi Ɗalibanka**

Mutum nawa ne suka samu rashin daidaito da iyayensa/mai kura da shi? Abokai?

Ku nawa kuke yin amfani da dandalin sadarwar zamani? Shin ka yi tunani a kan yanda mutane suka ɗaukin furofayil ɗinka na dandalin sadarwar zamani?

Shin ka taɓa goge wani abu ko cire maƙalakar da aka yi a cikin wani abun da ka raba a dandalin sadarwar zamanin (misali., hotuna, bidiyoyi, aike masu ɗauke da rubutu)? Me yasa?

# Bayyana Ra’ayi

## Kashi na Ɗaya

**Sanar da Ɗalibanka**

Yi tunani a kan hanyoyi daban-daban da mutane a rayuwarka suka san ka.

**Tambayi Ɗalibanka**

Shin ka taɓa aikata wani abu daban a gaban mutane wanda ya bambanta ka? Shin kana yin magana da iyayenka / masu kula da kai ko malamanka irin yanda kake yi da abokanka? Me yasa / me zai hana?

**Sanar da Ɗalibanka**

Dukkanmu mutane ne da muka ɗan bambanta dangane da inda muka fito da kuma wanda muke tare da shi.

A matsayin wani ɓangare na wannan aikin za mu tattauna a kan yanda za ka gabatar da kanka a intanet, musamman ma a dandalin sadarwar zamani, da kuma yanda wasu mutanen za su ɗauke ka ta hanyoyi daban-daban dangane da nasu ra’ayoyin.

**Tambayi Ɗalibanka**

Shin kana gabatar da kanka ta hanyar daban-daban a intanet ga mutane daban-daban? Misali, a wani dandalin (misali., Facebook) da za ka iya yin amfani da sunanka na ainihi, amma kana yin amfani da sunanka na ainihi wajen yin komai da komai a intanet?

Wasu dandalin sadarwar zamani ne yawanci ba ka yin amfani da sunanka na ainihi ko dandali-dandalin da kake ɓoye sunanka? Me yasa?

Shin kana ganin bayanin da ka raba a intanet game da kanka ya nuna yanda kake a zahiri? Shin kana ganin furofayil ɗinka na dandalin sadarwar zamani ya bayar da labarinka gaba ɗaya? Shin kana so su?

**Tambayi Ɗalibanka**

Ta yaya mutane za su dube ka idan suna da damar isa ga wasu daga cikin bayananka ne kawai? Misali, shin ra’ayin iyayenka’ / masu kula da kai’ zai canza idan suka ga duk abubuwan da ka aikata a wani dandalin sadarwar amma ba ka aikata a wani ba?

Ka taɓa sirrinta aikenka? Me yasa?

**Tambayi Ɗalibanka**

Mun yi magana a kan ra'ayi da yawa yau. Bisa la'aƙari da firarmu, wane abu guda ɗaya ne ka koya game da ra'ayi yau?

Wace hanya ce kuma ra'ayi ke shafar yanda muke kimanta bayani? Shin za ka iya faɗin sunan wani sha'anin kwanan nan a inda wannnan ya dace? Ta yaya ra'ayi ke da muhimmanci ba a rayuwarmu kawai ba, amma har ma da labarai su ma?

# Aiki

## Kashi na Ɗaya

### Aiki

Nemi mahalarta taron su:

1. Ɗauki hoton/hoton allon wani aike a dandalin sadarwar zamani [ma’ana., hoto, bidiyo, aike mai ɗauke da rubutu] (ba sai lallai nasu ba)

2. Bayyana rawa guda uku da aiken wani a dandalin sadarwar zamani ke takawa (misali., aboki, wani daga cikin iyali, malami), sannan kuma, a kowace rawa, a cikin taƙaitaccen sakin layi, yi bayani a kan yanda wannan mutumin zai ji game da wannan aiken.

A cikin aƙalla mintuna 10, rarraba mahalarta taron mutum bibbiyu, sannan ka nemi su raba aƙalla hanyoyi guda biyu tare da abokan aikinsu da suka yi imani cewa ra’ayi yana da muhimmancin aiken da suka zaɓa.

Wannan kayan karantarwar da Matasa da Kafar Watsa Labarai suka samar a Cibiyar Samar da Intanet &amp ta Berkman Klein; Jama'a a Jami'ar Harvard a ƙarƙashin lasisin Creative Commons Attribution-ShareAlike 4.0 International. Za ka iya yin amfani da wannan, har da yin kwafi da kuma shirya samar da ayyuka, ko kuɗi ko kuma wanda ba na kuɗi ba, kamar yanda ka siffanta. Matasa da Kafar Watsa Labarai a matsayin tushen da suka samar da ayyukan na ainihi da kuma raba wasu ayyukan da za su zo a gaba a ƙarƙashin sharuɗɗa ɗaya. Waɗannan da wasu ƙarin kayayyakin karantarwar su ma akwai su a intanet a Dandalin Kayayyakin Karatu da Rubutun Zamani na Berkman Klein.